MUJALLAR CITAD RADIO
RADIYON DA ZAKU SAURARA
www.citad.org/radio

Volume 3, issue 1

13-05-1443 AH
17-12-2021 AD


*CIBIYAR BUNKASA FASAHAR SADARWA DA CIGABAN AL'UMMA (CITAD) NA BAYAR DA HORO KAN ILIMIN NA'URA MAI KWAKWALWA*

## LABARAN CIKI

| | |
|---|---|
| **Muryar Matasa** | 1 |
| **Watch Dog** | 2 |
| **Ilimin 'Ya Mace** | 3 |
| Sharhin Yau da Kullum | 4 |
| **Shiri Na Mussamman** | 5 |
| **Siyasa Da Rayuwa** | 6 |
| **Ilimi Da Matasa** | 7 |

**Zaku iya sauraro da sauke manhajar CITAD RADIO ta wannan likau din dake kasa**



*https://play.google.com/store/apps/details?id=com.citad.org&hl=en&gl=US*

# An Rufe taron kaddamar da makarantar koyar da harkar sadarwa ga yan karkara.

An rufe taron koyar da harkar sadarwa na kwana na hudu da kaddamar da gudanar da makarantun al'umma na kananan kungiyoyi a Najeriya. Makarantar wacce ita ce irinta ta farko kuma kuma aka gabatar da ita a zahiri kuma za ta ci gaba da wakana.

Tun daga ranar farko da aka fara gudanar da ayyukan Spectrum na makarantun wanda Dr. Yusuf Abdulkadir ya gabatar da jawabinsa mai zurfi a kan spectrum da manufofinsa.
Yayin da rana ta biyu ta kasance gabatarwa akan TWSP daga Kabir S. Ahmed, an yi tambayoyi don a sami fahimi da fahimi game da abubuwan. A cikin zama na biyu na makarantun an raba mahalarta ko kuma a karkasa su gida uku don a gwada su tare da fito da wasu ra'ayoyi na abin da suka yi tunani.

Abdulhamid Bello daga Genuine System, ya dauki lokaci mai tsawo yana bayani da bayyana fasahar mahalarta gasar VSAT da kuma tsarin sanyawa a matsayin kashi na uku na makarantar. yana ɗaukar mahalarta ta hanyar Tsarin Manufofin ICT a Najeriya & Cibiyoyin Sadarwar Jama'a, ƙalubale ne da dama da ke kewaye da yanayin man-



ufofin.

Zama na hudu Engr. Usman Ma'aruf Yakubu kamar yadda babu wata takamaiman manufa da ke goyon bayan kafa cibiyoyin sadarwar jama'a a kasar nan kamar yadda ya fara, watakila zaman ya shafi bayanin manufofi da ka'idoji a cikin cibiyoyin sadarwar jama'a, da kuma abin da kananan kungiyoyi za su iya yi a matakinsu. don tallafawa aiwatar da manufofin hanyoyin sadarwar al'umma. Zama na biyar ya kasance gaba daya kan zabin Fasaha da tarihin fasahar sadarwa kamar yadda Engr. Rabi'u Haruna.

Zabin fasaha da bullowar Network Generation an yi shi ne a zaman taro na shida da na bakwai na makarantun wanda shi ma Engr. Rabi'u Haruna. An kuma nishadantar da tambayoyi da tsokaci a lokacin makarantun.

A karshen taron, Malam Haruna Adamu Community Network Project Coordinator Project ya yi alkawarin amfani da su tare da sauke abubuwan da suka koya a zahiri ga al'ummarsu.

Makarantun sun kasance wani ɓangare na Kunshin Aiki na 2 na Tsarin Tallafin Jama'a don magance Divide a Najeriya Project wanda Cibiyar Fasaha da Ci Gaba (CITAD) ke aiwatarwa tare da tallafi daga Ofishin Raya Commonwealth na Waje (FCDO) ta hanyar Association for Progressive Sadarwa (APC), ta ƙaddamar da Makarantar Sadarwar Jama'a ta Najeriya ta Farko don Kungiyoyin Kungiyoyi.

A manufar aikin ne don hada unconnected yankunan a Najeriya inda al'ada kasuwar 'yan wasa sami shi da wata riba da ya tura su networks da kuma manufar da School of Community Networks shine ginawa da-

# CIBIYAR CITAD TA KAI ZIYARA OFISHIN JAM'IYYAR PRP A KANO KAN SHIGAR MATASA SIYASA



Cibiyar bunkasa fasahar sadarwa da cigaban al'umma CITAD tare da hadin gwiwar Action Aid sun bayyana Haka ne a lokacin da suka Kai ziyara offishin jami'ar PRP dake kano.

Mal Isa Garba Wanda ya jagorancin tawagar ya bayyana kuduri CITAD na son ci gaban Kano da matasa a fanni siyasa inda yace wanna kuduri ne daga kungiyar Action Aid Nigeria inda zasu shiga cikin birni da kauyuka Dake fadin jahar don wayar da matasa da Mata Akan alfanu dake cikin shiga siyasa a wanna zamani tare da kawo sababin dabaru na tunkara zaben shekara 2023.

Shugaban jami'iyyar PRP Rashen jihar, Kano Comrade Sammani Sharif yabawa CITAD da ACTION AID bisa wanna kuduri inda ya ce matasa sun rasa wayenda zasu basu goyan baya wajen gani sun cimma muradan su na shiga fagen siyasa a jaha da kasa,Wanda tuni jami'ar PRP suka yaba tare da bada goyan baya akan wanna kokari na wayarwa matasa Kai daga kungiyar Action Aid

Cibiyar bunkasa fasahar sadarwar da cigaban al'umma CITAD tare da hadin gwiwar action aid zasu gudanar da wayenan ziyara a ofisusun shuwagabanin PDP da APC A jahar Kano.

# CIBIYAR CITAD TA FARA BAYAR DA HORO NA KWANAKI BIYU AKAN ALLURAR RIGA-KAFIN KORONA

.Cibiyar bunkasa fasahar sadarwar da cigaban al'umma CITAD tare da hadin gwiwar action aid zasu gudanar da wayenan ziyara a ofisusun shuwagabanin PDP da APC A jahar Kano.



A ƙoƙarinta na ganin ta wayar da kan al'umma akan muhimmancin da ke tattare da Allurar Riga-kafin korona, cibiyar bunƙasa fasahar sadarwa da cigaban al'umma CITAD, tare da tallafin gidauniyar MacArthur Foundation ta shirya wani taron horarwa ga mutanen da za su yi aikin wayar da kan al'ummar Najeriya alfanun da ke tattare da karɓar riga-kafin.

Mutanen da su ke karɓar horon sun fito daga jihohin Kano da Maiduguri da Bauchi da Kaduna. Sauran jihohin da mutanen su ka fito sun haɗa da Jihar Kogi da kuma Plateau.

Dr. Nura Ibrahim Malami a tsangayar sadarwa ta jami'ar Bayero da ke Kano, na daga cikin waɗanda ke bayar da horon.

Haka kuma ana sa ran cewa bayan kammala wannan horo na musamman waɗanda su ka amfana za su koma jihohinsu su cigaba da aikin wayarwa da al'umma kai akan muhimmancin allurar riga-kafin da kuma yaƙi da labarun karya da ake yaɗawa a game da riga-kafin.

# CITAD Na Cigaba Da Baiwa Mata Horo Na Musamman Akan Na'ura Mai Ƙwaƙwalwa





A ƙoƙarinta na ganin an dama da mata a cikin al'amuran rayuwa a ɓangarori daban-daban, Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Cigaban Al'umma (CITAD), na cigaba da baiwa mata horo na musamman akan yadda za su amfani da fasahar sadarwa wajen dogaro da kai a harkokin sana'o'in su.

Horon wanda hukumar raya al'adu ta Birtaniya da kuma tarayyar Turai su ka bayar da tallafi, yana mayar da hankali wajen koyar da mata yadda za su yi amfani da na'ura mai ƙwaƙwalwa a sana'o'in su tare kuma da ƙara samun gogewar da za su yi gogayya da zamani a harkar fasahar sadarwa.

Masana dai na kallon a duk lokacin da baiwa mata ilimin na'ura mai ƙwaƙwalwa tare da koya musu yadda za su yi sana'ar dogara da kai za su taka muhimmiyar rawa a fannin kimiyya da fasaha, kuma hakan zai matukar taimakawa a samu ci gaba a cikin al'umma.

# CIBIYAR CITAD NA CIGABA DA HORAR DA MATA ILIMIN



Abin gwanin ban sha'awa, yadda 'ya'ya mata, matasa, waɗanda a cikinsu har da 'yan mata da zawarawa da matan aure, dukkaninsu sun jeru reras a gaban malamarsu, Malama Halima Sa'idu Nayaya, tana koyar da su ilimin kwamfuyuta, da yadda za su inganta rayuwarsu ta hanyar amfani da kafar intanet.

Jaridar TheDailyReality (TDR) Hausa ta samu ganawa da wasu daga cikin matan da suka ci gajiyar wannan shiri. Ga kuma yadda hirar tamu ta kasance da ɗaya daga cikin ɗaliban da suka ci gajiyar shirin.

Gundarin hira:
TDR Hausa: Yaya sunanki?
Sunana Fauziyya Abdurrahman.
TDR Hausa: Me kika zo yi a nan?
Mun zo wani taron horo ne a CITAD na taimakawa mata da 'yan mata a kan wasu al'amura da suka shafi intanet ta yadda za a taimakawa mata, waɗanda za mu ƙaru da su a sana'o'inmu da sauran ɓangarorin rayuwarmu.

TDR Hausa: Ta yaya kika san za a yi wannan horon?
Gaskiya dai dama ce na samu, don ba wanda ya sanar da ni. Kawai ina danne-dannen waya ne sai naga shafin, sai na cike.

TDR Hausa: Ke da kanki kika gani?
Ni da kaina ne, ina danne-dannen waya ba tare da sanin kowa ba, kuma na cike. Kuma ga shi na samu.

TDR Hausa: Me da me kika koya daga fara wannan shirin?
Kamar yanzu na koyi abubuwa da dama. Ka ga ni yanzu ɗaliba ce a ABU Zariya, kuma na koyi yadda ake zane-zane. Kuma a yanzu zan iya rubutuna kundin digirina da kaina. Zan iya 'yan zane-zane a kwamfuyuta. Zan iya kula da sakamakon jarrabawata, ko da an cuce ni zan iya ganewa. Sannan kuma zan ƙarfafa amfani da intanet.

TDR Hausa: Kin yi maganar in an cuce ki, kina nufin za ki yi faɗa da malamanki kenan ko yaya?
Fauziyya: A'a, ina nufin kamar idan an yi kuskure wajen shigar da bayanai, zan iya ganewa kuma zan nemi haƙƙina yadda ya dace. Ba wai rigima da malamaina nake nufi ba.

TDR Hausa: Wane kira za ki yi ga mata da suke gida a zaune, kuma suna amfani da waya?
Fauziyya: A gaskiya suna rasa wata babbar dama. Ka ga kamar yanzu ni matar aure ce. Amma aure ba ya hana karatu. Ina kira gare su da suka dinga amfani da wayoyinsu wajen samun damarmaki kuma su yi amfani da su. Su yi amfani da wayoyinsu wajen abubuwan da za su taimake su kuma su taimaki al'umma.

TDR Hausa: akan yi amfani da waya wajen samun kuɗi, misali a ce ka bayar da dubu ɗaya za a ba ka dubu goma. Ta yaya za ki alaƙanta irin wancan abu da abin da kuke yi a yanzu?
Fauziyya: ai ba ma haɗi. Wancan ai damfara ne. Kuma suna amfani da rashin ilimin mutane ne da kuma son banzarsu. Amma wannan kuma ka ga ilimi ne da ake koyarwa a fili kiwa yana gani. Don haka ba haɗi a tsakanin biyun.

TDR Hausa: Me ye saƙonki na ƙarshe ga mata matasa?
Su dage a neman ilimi da duk abubuwa da za su taimaki rayuwarsu, domin in an san yau, ba a san ya gobe take ba.

TDR Hausa: Mun gode

WWW.CITAD.ORG/ RADIO

Main Office:3rd Floor, NSITF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 080-68078282
080-54362931
070-33427467
E-mail: info@citad.org,
Website: www.citad.org

www.citad.org

**Center For Information Technology and Development**

**BABBAN EDITA**
Hamza Ibrahim

**EDITA**
Buhari Abba Rano

**MATAIMAKIN EDITA:**
Gazzzali Haruna

**MAI KULA DA TSARE-TSAREi:**
Ali Sabo

**Mai Kula Da Dab'i**
Salim Sani Shehu

Zaka iya tura tura rahotan wani aiki wanda ya shafi al'umma, kai tsaye kamar, rowan sha, asibiti ko kuma makarantu da gwamnati bata gama ba zuwa CITAD dan samun damar shigar da kai cikin wandanda suka zama zakaran gwajin dafi kuma har ka samu kyautar kudi da computer.

